# Cibiyar Kayayyaki da Tallafi wato RSH ta Najeriya: Kayan aiki na binciken haɗari da gudanarwa a kan kiyayewa (ko SEAH)

Duk wata ƙungiyoyi masu zaman kansu(CSO) na fuskantar haɗarorin kiyayewa masu yawan gaske. Kuma, yadda yanayoyi, sauyi, dangantaka, da kuma haɗarori, na iya canzawa kan lokaci, binciken haɗari aiki ne na ko da yaushe (ba na lokaci daya ba ne).

Binciken haɗarin kiyayewa ko SEAH shine fifiko ga kowane matakin kiyayewa da martani na kowane kungiyoyi masu zaman kansu wato CSO. Cibiyar Kayayyaki da Tallafi wato RSH ta Najeriya ta samar da wannan kayan aikin binciken haɗarin kiyayewa da kayan aikin gudanarwa domin taimaka muku wajen gano da sarrafa haɗarorin kiyayewa da ƙungiyoyi masu zaman kansuke fuskanta.

Muna godiya ga ƙungiyoyin masu zaman kansu a Najeriya waɗanda suka gwada mana wannan kayan aikin, kuma muna maraba da ƙarin bayani - idan kuna son ba da ra'ayi kan abubuwan da kuka fuskanta da kuke amfani da wannan kayan aikin, ko kuma idan kuna da tambaya na wani takamaiman batu na kiyayewa, da fatan za a yi mana sakon imal: askanexpertnigeria@rshub.org.uk.

## An samar da wannan kayan aiki domin Ƙungiyoyin Masu Zaman Kansu a Najeriya, kuma zai yi amfani ga:

- Ma'aikatan da ke da alhakin kiyayewa ko PSEAH waton Kariya daga Cin da Gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i
- Ma'aikatan ɓangaren ɗaukar ma'aikata
- Ma'aikatan tsaro da haɗari
- Ma'aikatan shirin da ke aiki a kowane yanki/ɓangare na shirin
- Manajoji da daraktoci da ke lura da tsarin gudanarwa na haɗari

## Kafin ku fara, ku tuna:

➔ Mai yiwuwa a haɗa tsarin gudanar da haɗari tare da tsarin gudanar da haɗarin ƙungiyar da dama akwai shi. Ba ya buƙatar a raba shi.

- ➔ Wannan ba cikakken jerin haɗarori ba ne. Yanayin haɗari yana canzawa, ana buƙatar ku gano takamaiman haɗarorin kungiyarku.
- ➔ Cika binciken hadarin kiyayewa a karo na farko na iya zama tsari mai cin lokaci! Bayan haka za ku iya mayar da hankali kan sabuntawa da ƙari.
- ➔ Wasu hadarorin, misali a cikin muhallin da ke waje da wuraren haɗari na shiri, za su zo tare da binciken kariya na ƙungiyarku.

## Yadda ake amfani da wannan binciken hadari da kayan aikin gudanarwa:

**Mataki na 1**
- Binciki yadda kowane yanki mai haɗari ya shafi Kungiyoyi masu zaman kansu ta amfani da tambayoyi masu jagoranci
- Lura da haɗarori da ke cikin rijistar haɗari (duba samfurin RSH Nigeria da ke fayil na Excel)
- Kasafta haɗarori (Kaɗan, matsakaici, babba)

➔

**Mataki na 2**
- Gano hanyoyi ragewa da sarrafa haɗarorin
- Kasafta albarkatun da suka dace
- Dora alhaki da ƙayyadadden lokaci
- Rubuta matakan da aka ɗauka domin ragewa

➔

**Mataki na 3**
- Sa ido kan haɗarorin da matakan da aka dauka domin ragewa, misali bayan kowane wata 3
- Daidaita shirye-shirye da hanyoyi na ƙungiya inda ya dace

➔

**Mataki na 4**
- Sake duba *duk* nau'i na haɗari (ciki har da wuraren da aka fara ganin babu haɗari a tare da su), misali bayan kowane wata 3.
- Sabunta rijistar haɗari.

## Rarrabe haɗarori

A lokacin rarrabe haɗarin da aka gano, yana da amfani a yi la'akari da **yiwuwa** na faruwar (wato yiwuwar faruwar lamarin) da **tasiri** (yaya munin illar da zai iya jawowa ga dai-daikun mutane ko ƙungiyar).

| 1. Kula da yiwuwar faruwar haɗarin | |
|---|---|
| Mai matuƙar yiwuwa | 3 |
| Mai yiwuwa | 2 |
| Ba ya yiwuwa | 1 |

| 2. Kula da tasirin yiwuwar ga ɗai-ɗaikun mutane da sunan ƙungiyar | |
|---|---|
| Babban tasiri | 3 |
| Matsakaicin tasiri | 2 |
| Ɗan ƙanƙanin tasiri | 1 |

| 3. Kimanta ingancin haɗarin gaba ɗaya: yiwuwa x tasiri | |
|---|---|
| Babba | 7 zuwa 9 |
| Matsakaici | 4 zuwa 6 |
| Kaɗan | 1 zuwa 3 |

Mun kasa haɗarorin zuwa manyan sassa shida. Kuna iya gano sassan da suka dace da ku, amma ana ba da shawarar cewa an kula da manyan wuraren duka a cikin binciken haɗarinku. Danna domin samun zuwa kowane sashi.

**Akwai da yawa a nan! Zaɓi sashi ɗaya domin farawa. Da zarar kun gama wannan nau'in ku matsa zuwa na gaba. Kuna iya dawowa zuwa sashi na gaba wata rana/yayin da kuke da ƙarin lokaci.**


1. Muhallin waje, p3
2. Shirye-shirye, p5
3. Haɗin-gwiwa, p8
4. Sadarwa & Gudanar da bayanai, p8
5. Ɓangaren ɗaukar aiki da kula da ma'aikata, p10
6. Mulki, al'adu & shugabanci, p12


## 1. Muhallin waje

| # | Ɓangare mai haɗari | Dalilin haɗarin | Yaya wannan ya shafi aikin da kuke yi? |
|---|---|---|---|

| | | | |
|---|---|---|---|
| 1.1 | Shekaru | Kasashen da ke da ƙarancin shekarun amincewa da jima'i na ba da izinin yin jima'i da yara, wanda zai iya sanya su cikin haɗarin cin zarafi ta hanyar jima'i ko cin da gumi. Ba dole bane ma'aikata su lura da manuniya ta yiwuwar cin zarafi, don ana iya ɗaukar daidai suke da "al'ada." | * Shin shekarun amincewa a Najeriya/jihar XXX ya yi kasa da 18?<br>*Lura: amincewa ya shafi duk yayan da suka yi aure da marasa aure (ƙasa da 18)* |
| 1.2 | Hanyoyin lahani da cin zarafi | Ana iya ganin cin zarafi ko cin da gumi na wasu gungun yara ko manya a matsayin al'ada a cikin gida, kamar auren yara, cin zarafin don bambancin jinsi ko hukunci na jiki. Ma'aikata na iya yin imanin waɗannan ƙa'idoji abubuwan karɓa ne kuma su yi aiki da su. Wata ƙila sun ƙi jinin wasu yara (misali, yara masu nakasa) ko kuma ƙilan suna da imani mai rauni a kan cewa yara na iya amincewa da shiga cikin aiki na jima'i. | * Wadanne nau'o'i ko hanyoyi na cutarwa da cin zarafi (GBV, kare hakkin yara) ke samuwa a wuraren da kuke aiki?<br>* Shin akwai gungun na musamman na yara ko manya waɗanda suka fi haɗarin rauni? |
| 1.3 | Yanayi na Aikin Agaji | A lokuta na rauni, ƙila ba za a iya biyan muhimman buƙatun iyalai da al'ummomi ba yawanci kuma batutuwan kariya ko kiyayewa na ƙara tsananta. Suna iya zama cikin haɗarin cin da gumi ta hanyar jima'i da musanyar ayyukan jima'i domin samun abinci, mafaka ko tsaro. Iyalai da al'ummomi na iya kasawa wajen taimakon juna kuma ana iya samun rashin fannoni na tallafi ko ba sa aiki yadda ya kamata. A yayin da aka samu ɓarkewar hargitsi cikin gaggawa da ke buƙatar sa baki kai tsaye, ƙungiyoyi na iya daukar gajerun hanyoyi, kamar rashin gudanar da binciken usulin ma'aikata, ko rashin yin cikakken binciken haɗarori. Daukar waɗannan gajerun hanyoyi na iya lalata tsaro da aminci shirin. | * Shin halin da kuke ciki na hargitsi ne ko bala'i?<br>* Shin akwai mutanen a in da kuke aiki da suka yi gudun hijira ko kuma suka rasa dukiyoyinsu kuma ba za su iya biyan bukatunsu na yau da kullun ba, kamar abinci ko matsuguni? |
| 1.4 | Talauci mai tsanani | Kasancewa cikin talauci na iya sa mutane cikin raunin da zai sa a yi cin da gumisu ta hanyar jima'i da sa su musanyar ayyukan jima'i domin samun mahimman buƙatu daga al'umma da ma'aikata. Yara na iya yin aiki, kuma | * Shin talaucin ya yi tsananin da zai sa mutane za su iya fuskantar haɗarin cin da gumi ta hanyar jima'i ko cin zarafi don samun wasu kayayyaki? |

| | | | |
|---|---|---|---|
| | | ƙungiyoyi ko masu samar da su na iya amfani da aikin kwadago na yara. | |
| 1.5 | Yawan yara / manya da ke buƙatar kariya ta musamman | Ga yara (da manya) masu fama da nakasa, waɗanda ke ɗauke da cutar ƙanjamau wato HIV/AIDS, marayu, 'yan gudun hijira (IDPs), 'yan gudun hijira daga wata ƙasa ko waɗanda ke zaune a kan tituna, da dai sauransu. Haɗarin cin zarafi ya ƙaru saboda wani ɓangare na ƙyama, keɓewa, nuna bambanci da rashin tallafi. Ma'aikata na iya goyon bayan waɗannan son zuciyar kuma su kasa yin komai a yayin da suka ga cin zarafi. | * Shin akwai adadi mai yawa na yara ko manya da ke buƙatar kariya ko tallafi na musamman? |
| 1.6 | Mulki da aiwatar da doka | A yayin da aka samu rashin mulki na kwarai da aiwatar da doka, 'yansanda ko shari'a mai rauni mawuyaci ne a bayar da rahoto ko mayar da martanin rahotanni na cin zarafi. | * Shin hukumomi ko tsari na gida na amsa duka rahotannin cin zarafi ta hanyar jima'i, cin da gumi kobarazana?<br>* Shin hukumomin yanki na amsa wasu rahotanni amma ba sa amsa wasu rahotannin?<br>* Shin hukumomi ko tsarin gida na ɗaukar duka lamuran da muhimmanci? |
| 1.7 | Raunanan tsare-tsaren zamantakewa da kare yara | A yayin da aka samu raunanan tsare-tsaren zamantakewa ko kariyar yara, mawuyaci ne a dogara da sa bakin hukuma wajen lamuran amsa cin zarafi. | * Wadanne mahaɗar sada zumunci, lura da kuma tallafi ke samuwa ga manya da yara da ke cikin haɗari?<br>* Wdanne tsare-tsaren kariya da tsare-tsare na ƙasa, na gida da na al'umma ne suke aiki kuma a tanade kuma waɗannan suna aiki yadda ya kamata ga dukkan mutane? |
| 1.8 | Dabi'ar da ta shafi cin zarafin yara da mata | A inda aka jure tashin hankalin cikin gida da keta haddi ta hanyar jima'i ga yara da mata, mai yiwuwa ma'aikata ba za su iya sanin wannan cin zarafin ga mata, yara da sauran mutanen da ke cikin haɗari ba cewa hakan bai dace ba, ko kuma ba za su iya gane alamun cin zarafin ba. | * Wadanne halaye ake da su a kan tashin hankali ga mata ko yara a yankunan da kuke aiki?<br>* Shin tashin hankali ta hanyar jima'i, cin da gumi ko tozartawa al'ada ce a inda kuke aiki?<br>* Ana sauraren da kuma ɗaukar mutanen da suke magana da bayar da rahoto game da cin zarafi ta hanyar jima'i, cin da gumi ko barazana da mahimmanci? |

## 2. Shirye-shirye

| # | Ɓangare mai haɗari | Dalilin haɗarin | Yaya wannan ya shafi aikin da kuke yi? |
|---|---|---|---|
| 2.1 | Tsarin shiri | A inda babu buƙatu ko binciken haɗarin da ke kawo muryoyin masu rauni ciki har da mata, yara da mutanen da ke da nakasa, shirin ba shi da yiwuwar isar da manufofin da abubuwan da aka sa a gaba cikin aminci kuma yana iya ƙara haɗarin cutarwa. | * Shin ana tsara shirye-shirye ba tare da an gudanar da binciken haɗari ba?<br>* Shin ma'aikata ne kawai ke sanar da binciken haɗarin ban da al'ummomin da shirye-shiryen ya shafa?<br>* Shin dabarun rage haɗari an tsara su tare da haɗin gwiwar al'ummomi? |
| 2.2 | | Inda ba a tsara shirye-shirye daidai da ƙa'idoji da ksuka shafi kuma suka dace ba (misali Core Humanitarian Standards wato Muhimman Ka'idodin Aikin Agaji (CHS) ko ka'idar Do No Harm), shirin na iya saka mutane cikin haɗarin cin zarafi da gangan. | * Shin dabarun rage haɗari za su ba da damar shirin ya ci gaba cikin aminci kamar yadda zai yiwu amma har yana cimma manufofin?<br>* Shin shirye-shirye masu haɗari na musamman na ƙarƙashin shawarwari "mara yiwuwa" ko ƙarin kulawa domin ci gaba da tantance da sarrafa haɗari? |
| 2.3 | | A inda tsarin shirye-shirye da kasafin kuɗi ba su haɗa da abinda za'a kashe don matakan kiyayewa ba ko kuɗaɗe ba ya kai ga waɗannan matakan ba. | * Shin duk ayyuka da kudaden da za'a kashe kan kiyayewa an haɗa su cikin zayyana shirin da kasafin kuɗi?<br>* Shin akwai wasu byace-biyace da ba'a bayar na kuɗaɗen ba wanda zai iya kawo cikas ga amincin shirin? |
| 2.4 | Aiwatar da shiri | Inda ma'aikata da masu sa kai ke aiwatar da shirye-shirye waɗanda ba su fahimci cewa rukunoni na yara da al'ummomi daban-daban na fuskantar cutarwa da cin zarafi daban-daban kuma suna iya buƙatar nau'o'in sa baki na shirin daban-daban. | * Shin an horar da duk ma'aikata da masu sa kai da ke aiki kan shirin a kan kiyayewa da kuma yadda rukunoni daban-daban ke fuskantar haɗari?<br>*Shin dabarun rage haɗari za su yi aiki ga duka rukunoni daban-daban da ke cikin shirin? |
| 2.5 | | Inda ƙungiyoyi ba su da bambanci na ra'ayoyi kuma ba sa la'akari da yadda rukunoni daban-daban na yara da manya za su fi dacewa da shiga cikin ayyuka misali. ta | * * Shin ma'aikatan suna aiki akan shirin daga jinsi daya, kabila da dai sauransu? |

| | | | |
|---|---|---|---|
| | | rukunonin jinsi ɗaya, rukunonin nakasassu da dai sauransu. | * Shin yawancin ma'aikata ko kuma masu sa kai maza ne? |
| 2.6 | | A inda ba a sanar da wayar da kan jama'a game da kiyayewa ga mahalartar shirye-shirye da al'ummomin da aka yi niyya kan abin da za su iya tsammani daga ƙungiya da halayen ma'aikata da abokan aiki cikin harsuna da suka dace ba ko tare da kayan sadarwar da mahalarta shirin za su iya fahimta. | * Shin an yi ayyukan wayar da kan jama'a kan kiyayewa cikin yaren da ya dace tare da duka rukunonin al'umma?<br>* Shin wayar da kan jama'a yana nuna halayen da za'a iya tsammani daga ma'aikata?<br>* Shin al'ummomi sun san yadda ya kamata da kuma yadda bai kamata ma'aikata su nuna halayya ba? |
| 2.7 | Sa ido lura a kan shirye-shirye | Inda jama'a da mahalartar shirye-shirye ba su da hannu wajen sanya ido a kan shirin, ba za su iya tantancewa ko ana isar da shirye-shiryen ta hanyoyin da ke da illa ba. | * Shin ma'aikata ne kawai ke gudanar da ayyukan sa ido?<br>* Shin ana yin tambayoyi game da amincin shirin ko sa ido iyakancinsa cimma manufofin kawai? |
| 2.8 | | A inda ba sosai ake sa ido akan shiri ba, ba a saurin gano cutarwa da cin zarafi da wuri. | * Ana sa ido kasa da sau ɗaya a kowane watanni 3? |
| 2.9 | | A inda ƙungiyar ba ta da alamu na sa ido ko ana isar da shirye-shirye cikin aminci | *Shin akwai bayyanannun alamomi domin lura da cutarwa da cin zarafi da shirin ya haifar?<br>* Shin masu sa ido sun san yadda za su gane damuwa?<br>* Shin masu sa ido sun san yadda ake tambayoyi domin samun fahimtar ko ana isar da shirin cikin aminci? |
| 2.10 | Tsarin karbar shawarwari na al'umma (CFM) | A inda mahalarta shirin da al'umma ba su shiga cikin zayyana Tsarin karbar shawarwari na al'umma wato CFM ba, ba su da yiwuwar yin amfani da shi kuma tsarin na iya zama mara aminci ko samun cikas wajen biyan takamaiman bukatun rukunoni masu rauni a cikin al'umma kamar yara, mata, mutanen da ke da nakasa da sauransu. | * Shin an tsara hanyoyi kuma an sanar da al'umma Ko an yi zayyanar tare da al'ummomi?<br>* Shin shawara daga al'ummomi na haifar da canje-canje a cikin Tsarin karbar shawarwari na al'umma wato CFM ko shirin?<br><br>* Shin ƙungiyar tana bayar da shawara / amsawa ga al'umma game da yadda za su amsa rahoto da aka bayar? |
| 2.11 | | A inda Tsarin karbar shawarwari na al'umma wato CFM ba ta da tashoshi daban-daban misali layin waya da aka sadaukar, akwatunan korafe-korafe, sadarwa ta baki | * Akwai tashoshi daban-daban domin al'ummomi su koka? |

| | | | |
|---|---|---|---|
| | | domin biyan bukatu daban-daban na musamman ga masu rauni a cikin al'umma. | * Shin tashoshi daban-daban na bayar da rahoto sun dogara ne akan hanyoyin sadarwar da al'umma ke amfani da su? |
| 2.12 | | Idan ƙungiyoyi ba su da rubutattun manufofi/tsari wanda ke ƙunshe da jagororin abubuwan da za'a yi idan aka kawo tuhuma ko zargi ga ma'aikata ko jagorancin ƙungiyar, babu yiwuwar za su mayar da martani daidai da tsayuwa kan rahotanni da aka bayar | * Shin akwai jagororin bi da korafe-korafe da mayar da martani yadda ya kamata ga rahotannin da aka bayar na cutarwa da cin zarafi?<br><br>* Shin duka ma'aikatan sun san abun da za su yi idan sun samu rahoto? |
| 2.13 | | A inda ba'a kammala ko sabunta taswira ta duk hidimomin da ake buƙata domin mayar da martani ga rahotanni na cin zarafi, cin da gumi ko tozartawa na kowane wuri / yankin da kungiyoyi masu zaman kansu wato CSO ke aiki a ciki ba | * Shin akwai taswirar duk hidimomi, doka da hukumomi waɗanda za a iya amfani da su domin tallafawa ko tura wanda ya tsira zuwa inda ya cancanta? |

## 3. Hadin-gwiwa

| # | Ɓangare mai hadari | Dalilin hadarin | Yaya wannan ya shafi aikin da kuke yi? |
|---|---|---|---|
| 3.1 | Hadin-gwiwa | A inda aiki tare da abokan aiwatarwa yana da muhimmanci kuma kulawa ta ragu, misali saboda buƙatun gudanarwa daga nesa | * Shin abokan aiki ne kawai ke aiwatar da shiri ga baki daya ne ko kuma mafi yawa na cikin shirin?<br>* Ana sa ma abokan aikin ido akai-akai? |
| 3.2 | | A inda abokan aiki ba su san manufar kiyawewa da tsare-tsaren tafiyad da na ƙungiya ba | * Shin an binciki abokan aiki a kan iyawarsu na aiwatar da kiyayewa?<br>* Shin abokan aiki na da nasu manufofin da ka'idojin dabi'a waɗanda suka dace? |

| | | | |
|---|---|---|---|
| | | | * Shin yarjejeniyoyin da abokan aiki sun haɗa da kiyayewa? |
| 3.3 | | A inda babu ingantaccen horo da aka tsara ga abokan aiki, abokan aiwatarwa na iya sabawa dabi'u | * Shin akwai tsare-tsare da kudade domin horar da abokan aiki a kan kiyayewa yayin shirin?<br><br>* Shin ana bayar da shawara da tallafi ga abokan aiki a inda ya cancanta? |

## 4. Sadarwa da sarrafa bayanai cikin aminci

| # | Ɓangare mai haɗari | Dalilin haɗarin | Yaya wannan ya shafi aikin da kuke yi? |
|---|---|---|---|
| 4.1 | Sadarwa | A inda kayan sadarwar ba su kiyaye daraja da sirrin mahalarta shirin da al'ummar ba, mutane za su fuskanci haɗarin cin da gumi ta hanyar jima'i da cin zarafi | * Shin akwai jagorori na samu da buga hotuna da labarai ta hanyoyin da ba sa ƙarfafa ra'ayoyi mara kyau da tabbatar da gaskiya? |
| 4.2 | | Inda ba a samu izini a sane daga mahalarta shirin ba kafin amfani da hotunansu a cikin kayayyakin sadarwa na sa mutane ji kaman sun bambanta da wasu | * Shin ƙungiyar ta samu izini a sane misali mutanen da aka gabatar suna cikakken fahimtar yadda za'a yi amfani da bayanansu? |
| 4.3 | | Inda ba a samar da kayan sadarwa domin kiyaye mutanen da ke cikinsu cikin aminci ba, zai iya jefa al'umma cikin haɗarin cin zarafi ta hanyar jima'i da cin da gumi. | * Shin akwai jagororin samu da buga hotuna da labarai waɗanda ba sa amfani da cikakken suna da sauran bayanan da za su sa a gane? |
| 4.4 | | A inda sadarwa ba ta tayar da hankalin jama'a | * Shin sadarwa tana la'akari da duka masu iya karantawa da yadda za su iya fassara ko fahimtar abun ciki? |
| 4.5 | | A inda sadarwa ke amfani da harsunan da ba su haɗe kowa ba | * Shin harshen da ake amfani da shi a cikin gida ya dace kuma yana da amfani? |

| | | | |
|---|---|---|---|
| | | | * Shin amfani da wani harshe zai haifar da tashin hankali daga wasu masu karatu? |
| 4.6 | | A inda sadarwa ke sake "janyo" tunani mai rauni na cutarwa ko cin zarafi daga masu karatu | * Shin hotuna na bayyana tsiraici ne ko suna nuna cin zarafi ta hanyar da za ta iya dawo da tunani ko cin zarafi ko yanayi mai cutarwa? |
| 4.7 | Sarrafa bayanai cikin aminci da kariyar bayanai | A inda ba'a samar da tsarin don kiyaye bayanai daga al'ummomi/ma'aikata ba, wannan na iya sa su cikin haɗarin cin da gumi ta hanyar jima'i da cin zarafi, barazana ta hanyar jima'i, zalunci da haɓaka rashin kwarin gwiwa a kan tsarin | * Shin bayanai na ma'aikata da al'ummomi suna ajiye da kalmar sirri, ko akasin haka, wuraren adana bayanai masu kariya?<br>* Shin akwai tauye damar shiga waɗannan ma'ajiyar bayanai?<br>* Raba bayanai akan ma'aikata da al'ummomi yana ƙarƙashin ƙa'idodin kariyar bayanai?<br>* Shin duka ma'aikata sun san abin da ake nufi da tsare sirri kuma sun fahimci mahimmancin sirri game da waɗannan batutuwa? |
| 4.8 | | Inda ba a samar da tsari don kiyaye membobin al'umma da suka bayar da rahoto ba, mutane suna fallasuwa kuma ba za su so su bayar da rahoto ba | *Akwai rumbun adana bayanai guda ɗaya domin rahotanni da korafe-korafe waɗanda ke da kalmar sirri, ko akasin haka, mai kariya?<br>* Shin damar shiga wannan rumbun adana bayanai an tauye ga mutane da aka ambata sunansu waɗanda ke da alhakin kiyayewa da korafe-korafe/rahotanni? |

## 5. Bangaren ɗauka da kula da ma'aikata

| # | Ɓangare mai haɗari | Dalilin haɗarin | Yaya wannan ya shafi aikin da kuke yi? |
|---|---|---|---|
| 5.1 | Ɗaukar aiki | Inda ƙungiyoyi ba su da nassoshi domin tabbatar da ko asali na sababbin ma'aikata ko kuma inda binciken tushe | *Shin ana ɗauka masu shaidar nagarta biyu ko fiye ga ma'aikatan da suka yi nasara? |

| | | | |
|---|---|---|---|
| | | ba ya tambaya game da halayya da hali game da SEAH da kiyayewa. | * Shin masu shaidar nagarta sunyi la'akari da halin mutum da yadda yake kallon cin da gumi, cin zarafi da barazana ta hanyar jima'I wato SEAH?<br>* Ana duba shaidar bayanai na 'yansanda? |
| 5.2 | | A inda tambayoyi yayin ganawa domin sanin ilimi da sadaukarwa ga kiyayewa ba a haɗa su cikin tsarin daukar ma'aikata ba | *Shin ana tambayoyi yayin ganawa kan dacewar yin aiki tare da yara da al'umma da fahimtar kiyayewa? |
| 5.3 | | Inda tallace-tallace na aiki ba sa nuna ƙudurin ƙungiyar na rashin jurewarta ga cin da gumi, cin zarafi da barazana ta hanyar jima'I wato SEAH da sauran abubuwan da suka shafi kiyayewa a fili ba. | *Shin idan ana tallata duk ayyuka a ko ina, tallan yana haɗawa da duƙufa a kan kiyayewa? |
| 5.4 | | A inda ba a nemi ma'aikata su sanya hannu kan ka'idojin aiki da manufofin Kiyayewa ba | *Shin ana tambayar duk ma'aikata da masu sa kai su sanya hannu kan ka'idar aiki kuma su karɓi taƙaitaccen bayani a cikin yaren da ya dace domin su fahimci abin da suke sa hannu? |
| 5.5 | | Inda masu sa kai, ma'aikata na ɗan gajeren lokaci ko masu ba da shawara ba tare da la'akari da tsawon lokacin haɗin gwiwa ba a buƙaci su sanya hannu kan ka'idar aiki da manufar ƙungiyar a kan kiyayewa kuma ba su fahimci rashin jurewa ƙungiyar ga cin da gumi, cin zarafi da barazana ta hanyar jima'I wato SEAH ba | * Shin duk ma'aikata, ciki har da masu sa kai, haya na ɗan gajeren lokaci da masu ba da shawara, suna da taƙaitaccen bayani kan kiyayewa da sanya hannu kan ƙa'idar aiki? |
| 5.6 | Sarrafa gudanar da aiki | Inda ba a haɗa kiyayewa a cikin bayanin aikin ma'aikata ba kuma ba a yi bita sosai a kai ba yayin tsarin gudanar da aiki ba | * Shin duk bayanan aikin sun ƙunshi alhaki a kan kiyayewa?<br>* Shin ana sarrafa gudanar da aiki kuma wannan ya haɗa da tattaunawa a kan kiyayewa da damuwa da ma'aikatan za su iya samu tare da fahimtarsu ko iyawarsu wajen aiwatar da alhakin su a kan kiyayewa? |
| 5.7 | Wayar da kai | Inda ba a tsara horar da ma'aikata ba kuma ba a aiwatar da wayar da kai lokaci-lokaci a kan kiyayewa na ma'aikata ba | * Shin ana gudanar da horar da ma'aikata akai-akai kuma ya haɗa da kiyayewa?<br>* Ana gudanar da sabuntawa kowace shekara? |

| | | | |
|---|---|---|---|
| 5.8 | | Inda ba a bayar da damar tattaunawa akai-akai a kan kiyayewa ba | * Shin kiyayewa wani ajanda ce akan taron ƙungiyar? |
| 5.9 | | Inda ba a horar da masu sa kai ko ma'aikata na ɗan lokaci kan kiyayewa ba | * Ana horar da masu sa kai ko ma'aikata na ɗan lokaci a kan kiyayewa? |
| 5.10 | | Inda masu ba da shawara, 'yankwangila, wakilan kafofin watsa labarai da sauran wakilan ƙungiyar ba su samu wayar da kai game da manufofin kiyayewar ƙungiyar ba da rashin jurewarta ga cin da gumi, cin zarafi da barazana ta hanyar jima'I wato SEAH. | * Shin masu ba da shawara, 'yankwangila, wakilan kafofin watsa labarai da sauran wakilan ƙungiyar na samun taƙaitaccen bayani game da kiyayewa? |
| 5.11 | Bayar da rahoto | Inda ba'a tanadi tsare-tsare masu aminci da tsare sirri don ma'aikata su bayar da rahoto game da cin da gumi, cin zarafi da barazana ta hanyar jima'I wato SEAH ba | * Shin akwai tsarin da duk ma'aikata za su bayar da rahoton zato ko cin zarafi? |
| 5.12 | | Inda dukkan ma'aikata, masu sa kai da sauran wakilan kungiyar ba su san tsarin bayar da rahoton ma'aikata da kyau ba | * Shin duk ma'aikata sun san cewa an tanadi tsarin bayar da rahoto?<br>* Shin duk ma'aikata na jin daɗin amfani da tsarin bayar da rahoto dake tanade? |

## 6. Mulki, al'adu da shugabanci

| # | Ɓangare mai haɗari | Dalilin hadarin | Yaya wannan ya shafi aikin da kuke yi? |
|---|---|---|---|
| 6.1 | Al'ada da Shugabanci | Inda babu wani keɓaɓɓen mutum/wanda aka tantance masu jagorantar kiyayewa da tsarin aikin da ke bayyana halayyar da ake so daga matakin hukuma ko ma'aikata. | * Shin akwai masu jagorantar kiyayewa a matakin ma'aikata da masu jagorantar kiyayewa a Hukumar?<br>* Sun fahimci matsayinsu ko rawar da za su taka?<br>* Sun samu horo? |
| 6.2 | | Inda babu rijistar haɗari da gudanarwa da hukumar ke bita akai-akai ko rijistar haɗarin ba ta haɗa da kiyayewa ba | * Shin an haɗa kiyayewa a cikin rijistar haɗarin ƙungiya? |

| | | | |
|---|---|---|---|
| 6.3 | | Inda shugabannin sassa ba su da alhakin haɗa kiyayewa a ɓangaren da suke da alhaki a kai | * Shin shugabannin sassa sun fahimci rawar da tawagarsu ke takawa wajen kiyayewa?<br>* Shin suna tabbatar da cewa tawagarsu tana aiwatar da kiyayewa?<br>* Shin shugabannin sassan na da alhakin aiwatar da kiyayewa na tawagarsu? |
| 6.4 | | Inda manyan jami'an gudanarwa da hukuma ba sa bita ko sadar da manufofin ƙungiyar akai-akai | * Shin ana bitar manufar bayan kowace shekara 3?<br>* Hukumar ta sanya hannu a kai? |
| 6.5 | | Inda ba a haɗa matakan kiyayewa cikin hanyoyin tsara dabarun da ake da su ba | * Shin dabarun ƙungiyar sun haɗa da kiyayewa? |
| 6.6 | | Inda shugabanci ba ya aiki cikin gaggawa ko a bayyane ko bisa gaskiya bayan an kawo musu rahotanni ko zargin cin zarafi | * Shin shugabanci yana aiki cikin gaggawa ko a bayyane ko kuma a bisa gaskiya bayan an kawo musu rahotanni ko zargin cin zarafi? |
| 6.7 | | Inda rashin daidaituwa da nuna bambanci ga masu ra'ayoyi daban ya zama ruwan dare kuma ba a ɗau mataki a kai ba | * Shin rashin daidaituwa da nuna bambanci ga masu ra'ayi daban ya yaɗu?<br>* Shin ana ɗaukar mataki a kan rashin daidaituwa da nuna bambanci? |
| 6.8 | | Inda ake jan jiki ko hana magana a kan cin da gumi ta hanyar jima'i, cin zarafi da tozartawa ta hanyar jima'i | * Shin mutane suna magana a kan cin zarafi ta hanyar jima'i, cinda gumida tozartawa ta hanyar jima'i?<br>* Shin mutane na ja da baya daga yin magana da bayar da rahotanni na cin zarafi ta hanyar jima'i, cinda gumida barazana ta hanyar jima'i? |
| 6.9 | Bayar da Rahoto / Bincike | Inda daftarin manufofi/tsari bai ƙunshi jagorori kan abin da za a yi idan rahoto ya keta iyakokin iyawar ƙungiyar ba | * Shin akwai tsari kan abin da za'a yi idan ƙungiyar kadai ba za ta iya sarrafa wani rahoton da aka bayar ba?<br>*Shin akwai binciken haɗari ga kowane lamari da aka karɓa da tsarin tallafawa ko mayar da martani? |

RESOURCE & SUPPORT HUB

UKaid from the British people

| | | | |
|---|---|---|---|
| 6.10 | | Inda kungiyar ba ta iya sarrafa korafe-korafe cikin aminci ba misali kungiyar ba ta da kwarewar gudanar da bincike ko sanin inda za ta samu tallafi a waje | * Shin akwai tsarin mayar da martani a bayyane tare da alhaki?<br><br>* Shin ƙungiyar ta san inda da kuma lokacin da zai fi dacewa amfani da masu bincike daga waje? |

Wannan daftarin an fitar da shi ne daga aikin da Burtaniya ta bayar da tallafi (UK Aid) daga gwamnatin Burtaniya. Amma,
ra'ayoyin da aka bayyana da bayanai da ke cikinsa ba lallai ba ne na ko kuma an samu amincewa daga Gwamnatin Burtaniya ba wacce ba za ta iya karɓar alhakin irin waɗannan ra'ayoyi ko bayanai ko kowane abun dogaro ba
da aka sanya a kansu.

An shirya wannan wallafa domin jagora ga kowa game da sha'anin da ake magana akai kawai, kuma baya zama shawara ta ƙwararru. Bai kamata a yi aiki da bayanai da ke cikin wannan wallafar ba
ba tare da samun takamaiman shawarar kwararru ba. Ba a bayar da wakilci ko garanti (bayyananne ko wanda aka yi nufi) dangane da daidaito ko cikar bayanan da ke cikin wannan wallafar ba, kuma, gwargwadon yadda doka ta ba da izini, babu wata ƙungiya ko mutum da ke da hannu wajen samar da wannan takarda da ya karɓi ko ɗaukar wani alhaki, nauyi. ko kuma aikin kula da duk wani sakamako na duk wanda yayi aiki, ko ƙin yin aiki, dangane da bayanan da ke cikin wannan wallafar ko kuma ga duk wani da ya yanke shawara dangane da shi.